# Takardar aiki ta 1 ta Kimannta Lamurran da ke kawo VE

## Takardar aiki ta 1 a:

Layukan Tambaya a ƙasa za su taimaka muku gano lamurran da ke kawo VE masu alaƙa da muhallinku. Za a iya amfani da takardar aiki ta biyu domin amsa tambayoyin da ke ƙasa. An samo wannan takardai aiki ne daga Jagora ga Lamurran da ke kawo Tsattsauran Ra'ayin Rikici na USAID. Lamurran da ke turawa ko janyowa za su iya bambanta daga mutum zuwa mutum, saboda yana da kyau a yi la'akari da yadda lamurran da ke turawa da janyowa ke shafar mabambantan rukunonin mutane, da kuma duba tsare-tsare na lamurran da ake yawan samu a cikin waɗannan rukunoni. Fahimtar waɗannan bambance-bambance yana da muhimmanci, saboda za su bayyana yadda za ku tsara furojet-furojet ɗinku.

### LAYIN TAMBAYA NA 1: Muhalli Mai Kyau

Samar da fahimta ta yanayin rikici wanda shiga tsakani zai iya aukuwa. Domin manufar kimantawa, ba shi da wani muhimmanci samar da fahimta ta sosai ga dukkan lamurra masu tsari da ke kai wa ga VE, amma yana da muhimmanci a gano abubuwan yanayi da suke da alaƙa da muhalli wanda a cikinsa ne za ku gudanar da furojet. Yana kuma da muhimmanci gano waɗannan lamurra masu tsari da za su iya kai wa muhalli mai kyau domin VE, amma watakila furojet ɗinku ba sai ya nemi sauyi ba. Wannan zai taimaka matuka wajen bayyana haɗurra da hasashe a lokacin tsarawarku.

- [ ] A ina ne ake son VEOs su yi aiki? Wannan zai iya haɗawa da wuraren da ba a shugabanci ko ake shugabancin da bai dace ba, inda VEOs suka sami gindin zama, suke gudanar da horaswa da shirya hare-hare, da wuraren da ke fuskantar ayyukan VEO na ɗaukar ma'aikata. Waɗannan wurare za su iya kasancewa keɓaɓɓu, yankuna marar mutane masu yawa, ko wurare masu tarin jama'a, wurare masu sha'awa.
- [ ] Waɗanne lamurra ne a waɗannan yanaye-yanaye masu tsari da za su iya shiryawa da ba da gudummuwa ga tsattsauran ra'ayin rikici? A yayin da kuke son mayar da hankali ga takamammen yanayinku, watakila yana da kyau ku fahimci lamurra a matakin ƙasa, yanki, da gida, sannan da yadda suke da alaƙa da juna. Waɗannan za su iya haɗawa da danniya, cin hanci, rashin aiki, rashin daidaito, nuna wariya, kiyayya tsakanin ƙungiyoyin bayyana juna, shigar tsakani daga waje na ƙasa a lamurran da suka shafi wasu ƙasashe, da sauransu.
- [ ] Daga cikin lamurran da aka bayyana a sama, wanne ne mafi dacewa da yanayin da shirinku zai yi aiki a kai? Ta yaya sannan me ya sa?
- [ ] Ko waɗannan lamurra sun bambanta tsakanin maza, mata, yara maza da mata? Ko waɗannan lamurra sun bambanta tsakanin ƙungiyoyin ƙabilu da na addinai? Ta yaya sannan Me ya sa? Waɗannan za su iya haduwa da lamurran da ke turawa da aka bayyana a ƙasa.

### LAYIN TAMBAYA NA 2: Lamurran da ke turawa

Muhimmanci ga fahimtar matakin tsattsauran ra'ayi da abin da ke sa mutum shiga VEO ko ya ji yana shauƙin sa wa kansa tsattsauran ra'ayin rikici.

- [ ] Ko akwai **lamurran da suka shafi zamantakewa da tattalin arziki** a naku yanayi da suka yi tasiri ga wani mutum wajen shiga VEO ko aikata VE? Alal misali, ko kun ga wani tsari na shigar da mutane da mayar da su saniyar ware, nuna bambanci a tsakanin mutane, tsammanin da bai dace ba ko danne wa ɗan'uwa haƙƙi waɗanda za su iya kai wa ga tsattsauran ra'ayi ko yin tasiri ga mutum ya shiga VEO?
- [ ] Ko akwai **lamurran da suka shafi siyasa** a naku yanayi da suka yi tasiri ga wani mutum wajen shiga VEO ko aikata VE? Ko waɗannan lamurra sun taimaka wajen kawo tsattsauran ra'ayi a naku yanayi, ta yaya sannan me ya sa?
  - Ko akwai wani haƙƙi nan siyasa ko na bil'adama da aka danne, mummunar danniyar gwamnati ko mummunan saba wa haƙƙin bil'adama? Ko gwamnatinku tana da dama ko waɗannan ma'aikatu sun bata sunan inda mutane za su iya koma wa VE a maimakon hanyoyin siyasa domin samar da sauyi? Haka kuma, ko akwai lamurran da suka shafi cin hanci da rashin yin hukunci ga mutanen da ke da uwa a gindin murhu?
  - Ko akwai hanyoyi na doka domin sulhunta jayayya da yin gaskiya?
  - Ko akwai tsoratarwa ko cilastawa daga VEOs da za su iya matsa wa mutane shiga harkokinsu a inda gwamnati ba ta iya samar da kariya ga 'yan ƙasarta?
  - Ko akwai mamaya daga ƙasashen waje da/ko mamayar sojoji da za ta iya zama abun da ke tausaya wa VE ko ƙara shi? Ko akwai tunanin cewa tsarin ƙasashen waje bai yi adalci ba sannan yana ƙiyayya da ƙungiyoyinsu na addini da na ƙabilanci?
- [ ] Ko akwai lamurran da suka shafi al'adu a naku yanayi da suka yi tasiri ga wani mutum wajen shiga VEO ko aikata VE? Alal misali, ko akwai labarai ko tunanin jin cewa addinin wani ko ƙabila yana ƙarƙashin takurawa?

- Ko mutane na fuskantar baraznar da ta shafi al'adu, gargajiya, kyawawan ɗabi'u, da girma da mutunci na wasu mutane ko ɗaiɗaikun mutane?
- Ko lamurran da suka shafi zamantakewa da tattalin arziki, siyasa da al'adu sun bambanta tsakanin maza, mata, yara maza da mata? Ko waɗannan lamurra sun bambanta tsakanin ƙungiyoyin ƙabilu da na addinai? Ta yaya sannan Me ya sa?

**LAYIN TAMBAYA NA 3: Dalilan da ke Janyowa**

Muhimmanci ga fahimtar matakin tsattsauran ra'ayi da yadda mutane ke shiga VEO ko aiki da tsattsauran ra'ayin rikici.

- A al'ummominku, ko akwai masu tsattsauran ra'ayi da ake koyi da su? Wannan zai iya haɗawa da shugabannin addinai da ɗaiɗaikun mutane daga hulɗayyar zamantakewar mutane tare da ƙungiyoyin VE, da sauransu. Yaya suke ɗaukar mutane (misali, waɗanne labarai aka yi amfani da su a naku yanayi wajen ɗaukar mutane aiki, ko akwai mabambantan labarai da suke harin adadin mutane daban-daban)? Ko hanyoyin ɗaukar mutane sun sauya daga lokaci zuwa lokaci?
- Ko mutane a cikin al'ummarku suna haɗuwa da al'ummomin da ke da tsattsauran ra'ayi ta intanet? Waɗanne dandalin sadarwa suke amfani da su wajen sadarwa da masu yin tasirin shiga tsattsauran ra'ayi da ɗaukar mutane?
- Memutane suke neman samu daga shiga VEOs ko ɗaukar tsattsauran ra'ayin rikici? Alal misali, suna neman wata manufa ne (da aka samu ta hanyar aiwatarwa ta amfani da tunanin masu tushe), shirin ƙwarai, jin ana damawa, karbuwa, matsayi, sha'awar kayayyaki, tsoron sakamako daga ƙungiyoyin VE, ladan da ake tsammani bayan rayuwa, da sauransu.
- Ko VEOs da ɗaiɗaikun mutane da suke da tsattsauran ra'ayin rikici suna samar da mafita ga mutanen da dama suke cikin rikici wadanda suke neman kare halayensu na rikici?
- Ko waɗannan lamurra sun bambanta tsakanin maza, mata, yara maza da mata? Ko waɗannan lamurra na da bambanci a tsakanin ƙungiyoyin ƙabilu da na addinai? Ta yaya sannan Me ya sa?

Wannan takardar aiki ta zo bayan ta farko sannan za a iya amfani da ita domin amsa tambayoyin da ke sama.

| Sharhin Lamari | | Ta yaya waɗannan suka bambanta tsakanin maza, mata, yara mata da maza, ko ƙungiyoyin ƙabila da addini? |
|---|---|---|
| Muhalli Mai Kyau | | |
| Dalilan da ke Turawa | | |
| Dalilan da ke Janyowa | | |